# Shimfiɗar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ta kasance ta jemammiyar fata ce, cikinta kaba ne

Daga Nana A'isha uwar muminai - Allah Ya yarda da ita - ta ce: Shimfiɗar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ta kasance ta jemammiyar fata ce, cikinta kaba ne, a Riwayar Muslim kuma : Matashin kai na Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - wanda yake dogara a kan shi ya kasance na jemammiyar fata ne, cikinta kaba ce.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Uwar muminai Nana A'isha - Allah Ya yarda da ita - ta bada labarin cewa shimfiɗar da Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yake kwanciya a kanta ta kasance an yi ta ne da jemammiyar fata, kuma a cike ta ke da kaba ta dabino, haka ma matashinsa wanda yake kishingiɗa a kansa.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65820